# SHAYAR DA NONON UWA ZALLA-LAM



## Yaya Shayar Da Nonon Uwa Zalla Ke Aiki?

- Yana dakatarda kwayoyin haihuwa na diya mace. Wanan yana nufin ba kowane wata mace zata saki kwai ba. Idan kwai bai fito ba ya hadu da maniyi, kenan chiki bazai shiga ba.

## Fa'idar Amfani Da Wannan Dabarar

- Zaa iya anfani da wannan hanyar da zaran mace ta haihu
- Baya hana jima'i
- Babu bukatar kudi ko wani abu
- Yana dakatar da jinin al ada ga wasu mata
- Shayar da Nono Zalla yana ba jariri abinci mafi inganci

## Chikakken Bayani:

- Shayar da nono zalla hanya ce ta tazarar haihuwa na takaitaccen lokaci.
- Hanya ce mai inganci idan an tsare wadannan ka'idoji guda uku:
  - Idan mace tana da jariri kasa da wata shida da haihuwa
  - Idan mace tana shayar da jaririn nono zalla (dare da rana) ba tare da bayar da ruwa ko wani abinci ba
  - Idan bata ga jinin al ada ba tun bayan haihuwa.

## Yaya ingancin shayar da nonon uwa Zalla yake?

- Tabbacin aikin wannan dabarar ya kai kasha tamanin da takwas (98%) A chikin kasha dari (100%)
  Wato a cikin mata dari (100) da suka shayar da nono zalla guda biyu zasu samun juna biyu chikin wata shidda na farko bayan haihuwa.

## Motsawar Jiki Ko Laulayin da ake fuskanta:

Bashi da matsala

## Waye ba zai iya amfani da shayar da nonon uwa zalla ba?

Mace wadda:

- Keda yaro da ya wuce wata shidda da haihuwa
- Jinin al ada ya dawo mata
- Ta fara ba ma jaririn ta ruwa ko wani abinci yayin da take shayar da shi.

## Wa zai iya amfani da Dabarar Shayar da Nonon Uwa zalla?

Mace wadda

- Take cikin wata shidan farko bayan haihuwa, wato bata wuce wata shida da haihuwa ba
- Jinin al ada bai dawo mata ba bayan haihuwa
- Bata shayar da jaririn ruwa ko madara ba sai nono zalla dare da rana

**A KULA**
**Idan matar nada matsala da shayar da nono, yana da kyau ta ziyarci kwararrun ma aikatan asibiti su duba ta.**

*Get it together*
KNOW. TALK. GO.

NURHI 2
NIGERIAN URBAN REPRODUCTIVE HEALTH INITIATIVE

